# Muhimman Ka'idodin Aikin Agaji akan Inganci da Ɗaukar Nauyi

**Wallafawar:** CHS Alliance, Group URD da Sphere Project.

**Bugun Farko:** 2014

Wannan wata fassarar ce da hukumar ba ta amince da ita ba daga asalin ta Turancin, wadda CHS Alliance, Groupe URD da Sphere suka wallafa a baya. Waɗannan ƙungiyoyi ne suka yi fassarar da kansu wato: Social Development Direct da Translators without Borders. Ma'aikatan CHS ba za su ɗauki nauyin ingancin da daidaiton wannan fassarar ba.

© An kare hakkin mallaka. Hakkin mallakar abinda ke rubuce a cikin nan na CHS Alliance, Group URD da Sphere Project ne. Za'a iya kara bugawa don dalilan ilimi, har da don ayyukan horo, bincike da shirye-shirye, matukar za'a ambaci Muhimman Ka'idodin Aikin Agaji akan Inganci da Ɗaukar Alhaki a matsayin mai hakkin mallaka. Don fassara ko daidaita duk ko kowane ɓangare na Muhimman Ka'idodin Aikin Agaji akan Inganci da Ɗaukar Alhaki, dole ne a sami rubutaccen izinin ta tura imal zuwa info@corehumanitarianstandard.org

## Gabatarwa

Muhimman Ka’idodin Aikin Agaji akan Inganci da Ɗaukar Nauyi (CHS) wani sakamako ne na Gamayyar Kungiyoyi domin tabbatar da Inganci wato Joint Standards Initiative (JSI) a inda Gamayyar Kungiyoyin Agaji akan Ɗaukar Nauyi wato Humanitarian Accountability Partnership (HAP) ta duniya, da Mutanen da suke Aikin Agaji wato People in Aid da ƙungiyar Sphere Project suka hada karfi domin samun fahimtar juna/karfafa haɗin kai tsakanin masu amfani da ka’idojin aikin agaji. JSI ta tuntubi sama da ma’aikatan agaji 2,000 a manyan ofisoshi, yankuna da wuraren da suke cikin hatsarin bala’i na ƙasashe daban-daban. Bayanin da aka samu ya nuna buƙatar daidaita ka’idodin tare da garuruwa da mutanen da rikicin ya shafa a tsakiya da kuma la’akari da ka’idodin jin kai a matsayin tushen.

CHS sakamakon tattaunawa ne na wata 12 a matakai uku, a inda ma’aikatan agaji, garuruwa da mutanen da rikici ya shafa, daruruwan kungiyoyin tallafi masu zaman kansu (NGOs), da abokan aiki, gwamnatoci, ƙungiyoyin Majalisar Dinkin Duniya (UN) da masu ba da tallafi, da kuma masanan ilimi suka yi nazari sosai akan abinda CHS ya kunsa kuma suka jarraba aiki da shi a manyan ofisoshinsu da kuma fagen aiki.

Anyi la’akari da shawarwarin da aka samu daga kowacce tattaunawar, sannan gyaran da aka samu ya samu karɓuwa a wajen Ƙungiyar Kwararru masu Ba da Shawara na mutane sittin da biyar daga ɓangarori daban-daban na kwarewa a aikin agaji da samar da ka’idoji.

Kudiri ne na mashawartar HAP ta duniya, People In Aid da Sphere Project cewa CHS zai maye gurbin ka’idojin HAP na 2010 akan Ɗaukar Nauyi da Gudanar da Ingantaccen Aiki, Dokokin Dabi’u masu Kyau a lokacin Gudanarwa na People in Aid da ɓangaren Tallafawa Ma’aikatan Agaji da Muhimman Ka’idodi na Littafin Hannu na Sphere.

## Godiya

Godiya ga daruruwan ƙungiyoyi da ɗai-ɗaikun mutane da suka shiga a lokacin haɗa CHS ta ba da shawarwari akan rubuce-rubuce na CHS, ta gwada shi a cikin ƙungiyoyinsu[1], ko ta halartar ɗaya daga cikin rukunonin da suka jagoranci tsarin tattaunawa akan CHS. An yaba musamman shigowa da al'umma daban-daban da mutanen da rikici ya shafa a wajen tattaunawa da gwaji.

A ƙoƙarinsu na daidaita ka'idoji, ƙungiyar HAP ta kasa da kasa, People In Aid da Sphere Project sun hada da Groupe URD wadanda suka shigar da tsarin Quality COMPAS a cikin CHS. Ƙungiyar masu ba da shawara ta kwararru ta CHS da rukuninta, Kwamitin Aiwatarwa na Kwararru - Technical Steering Committee, sune da nauyin kula da tsarin shawarwarin da kuma amincewa ta ƙarshe ta CHS. An sake dorawa gungun waɗanda suka rubuta CHS da alhakin sake duba CHS don su shigar da shawarwarin da aka samu a kowane matakin tattaunawar.

Don tabbatar da cewa sakamakon da aka cimma ya kasance tare da kowa, ya wakilci ra'ayoyin mutane da manufa, tsarin tattaunawa na CHS an saukaka shi ta wasu mashawarta masu cin gashin kansu wato WolfGroup Consultants.

Za'a sami cikkaken jerin sunayen mambobin Ƙungiyar Kwararru masu ba da Shawara wato Technical Advisory Group, Ƙungiyar Kwararru masu Aiwatarwa wato Technical Steering Group da Ƙungiya kan Rubutu a www.corehumanitarianstandard.org. Ba don gudumawarsu da rashin gajiya wajen bada taimako ba, da tsarin tattaunawa na CHS ba zai yiwu ba.

An tallafawa tsarin Muhimman Ka'idodin Aikin Agaji da kuɗin muhimman aiki daga waɗannan masu ba da tallafi: Hukumar Harkokin Waje da Kasuwanci na Gwamnatin Austaraliya; Hukumar Katolika ta Bunƙasa Kasashen Waje (CAFOD); Hukumar Harkokin Waje ta Kasar Denmark (Danida); Ofishin Harkokin waje na Jamhuriyar Tarayyar Jamus; Taimakon Irish; Hukumar Hadin Gwiwa don Bunƙasa Kasa da Kasa ta Sweden; Hukumar Bunƙasa da Haɗin Gwiwa ta kasar Switzerland; Tallafin Burtaniya daga Gwamnatin Burtaniya; da Gwamnatin Amurka.

[1] Cikkaken jerin sunayen ƙungiyoyin da suka gwada CHS na samuwa a www.corehumanitarianstandard.org

HAP International, People In Aid da Sphere Project suna so su godewa waɗannan mashawartan don gudunmawar kuɗi da suka bayar don tsarin CHS: ACT Alliance; Action Aid International; Aktion Deutschland Hilft; Red Cross ta Burtaniya; Hukumar Katolika don Bunƙasar Ƙasashen Waje (CAFOD); CARE International; Christian Aid; Community World Service Asia; DanChurchAid; The Lutheran World Federation; Save the Children International; Save the Children US; da World Vision International.

## Shawarwari

Muna maraba da tsokaci akan CHS a kowane lokaci, kuma za'a iya tura su tare da tambayoyi, zuwa info@corehumanitarianstandard.org

## Bita

Dukkannin tsokaci ko bayanin da aka karba za'a yi amfani da shi wajen gyaran CHS da za'a yi kafin ƙarshen watan Disamba 2019. Domin ƙarin bayani akan Muhimman Ka'idojin Aikin Agaji tare da, da abinda ya danganci haka da sauran takardun da ake kan haɗawa, a ziyarci www.corehumanitarianstandard.org

## Tsokaci akan fassara

Za'a samar da Muhimman Ka'idojin Aikin Agaji a harshen Larabci, Faransanci da Spanish. Idan kuna son fassara CHS zuwa ƙarin harshe, don Allah tuntuɓi info@corehumanitarianstandard.org don jagora kan fassarar. Dukkan fassara kyauta ce, kuma za'a iya samunta a www.corehumanitarianstandard.org

## Abubuwan da suka shafi wannan

Akwai jagoranci da abubuwan da za su taimaka wajen tallafawa aiki da CHS kuma za'a iya samun su kyauta a www.corehumanitarianstandard.org

# Abubuwan da ya Ƙunsa


i. Gabatarwa 2 - 4

ii. Tsarin Muhimman Ka'idojin Aikin Agaji akan Inganci da Ɗaukar Nauyi (CHS) 5

iii. Aiwatar da CHS 6 - 7

iv. Iƙirari 7

v. Aikin Bada Agaji na Ka'ida 8 - 9

vi. Alkawura Tara da Ka'idodin Inganci 10 - 11

vii. Alkawura, Matakai da Ɗaukar nauyi 12 - 22

1. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa sun samu taimako da ya dace da buƙatun su. 12
2. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa sun samu damar taimakon agaji da suke buƙata a lokacin da ya dace. 13
3. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa ba su zama cikin kunci ba kuma a shirye suke, ga juriya kuma basu kasance cikin hatsari sakamakon ayyukan agaji ba. 14 - 15
4. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa sun san hakkinsu da abinda yake nasu, suna da damar samun bayanai da kuma shiga yanke shawarwarin da suka shafe su. 16
5. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa suna samun damar hanyoyi masu tsaro da samun amsa don magance korafe-korafe. 17
6. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa suna samun taimako da aka daidaita, kuma masu karfafawa juna. 18
7. Garuruwa da mutanen da rikicin ya shafa za su iya tsammanin ƙarin ingancin taimako tunda ƙungiyoyin agaji suna ɗaukan darasi daga ayyukansu da tunanin yadda za'a gyara. 19

8. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa suna samun taimakon da suke buƙata daga kwararrun ma'aikata da masu sa kai da ake kula da su da kyau 20

9. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa na iya tsammanin cewa ƙungiyoyin da ke taimaka musu suna sarrafa albarkatu tare da inganci, yadda ya kamata kuma cikin ɗa'a. 21 - 22

**viii.** Kamus **23 - 24**

# Muhimman Ka'idojin Aikin Agaji akan Inganci da Ɗaukar Nauyi

## i. Gabatarwa

Kowace rana a faɗin duniya, mutane da yawa daga kowane ɓangaren rayuwa suna jin ɗaukan mataki don amsawa hakkin taimakawa bil'adama idan suna cikin wahala – wato sha'awar hana da magance wahalar bil'adama a duk inda ta faru.

Muhimman Ka'idojin Aikin Agaji akan Inganci da Ɗaukar Alhaki (CHS) ta bada Muradai guda Tara wanda ƙungiyoyi da ɗai-ɗaikun mutane da suke aikin agaji za su yi amfani da su don karfafa inganci da tasirin taimakon da suke bayarwa. Yana kuma taimakawa wajen ƙara ɗaukan alhaki ga al'ummomi da wadanda rikici ya shafa: sanin abubuwan da ƙungiyoyi suka yi alƙawarin yi zai sa su riƙe waɗannan ƙungiyoyi da laifi idan ba su yi ba.

CHS tana sanya al'umma da mutanen da rikicin ya shafa a tsakiyar ayyukkan jinkai da kuma karfafa darajanta asalin hakkokin su a matsayin bil'adama. An kafa ta cikin hakkin rayuwa da mutunci, da hakki na kariya da tsaro kamar yadda yake a cikin dokokin kasa-da-kasa, har da Dokar Kasa da kasa ta 'Yancin Dan-Adam.[2]

A matsayin muhimmiyar ka'ida, CHS ta bayyana abubuwan da suka zama dole don aikin agaji mai ka'ida, ɗaukan alhaki da kuma mai inganci sosai. Ƙungiyoyin agaji na iya amfani da shi a matsayin wata ka'ida ta daidaita hanyar tafiyar da tsarinsu na cikin gida. Za'a iya amfani da shi kuma a matsayin wani tushena tantance ingancin ayyuka, wanda an haɗa wani tsari na musamman da manuniya da suka dace domin tabbatar da cewa zai yi amfani a yanayi daban-daban da ƙungiyoyi iri-iri.

[2] Dokar 'Yancin Kasa da Kasa ta hada da Sanarwar Kasashen Duniya game da Hakkin Bil'adama, Yarjejeniyar Duniya akan Hakkokin Tattalin Arziki, Zamantakewa da Al'adu, da kuma Yarjejeniyar Duniya akan Hakkokin 'Yan Farar Hula da Siyasa da Karin Ka'idodi na zaɓi.

CHS tana iya samun karfafawa da aiwatarwa daga ɗai-ɗaikun mutane, ƙungiyoyi, ƙungiyoyin da suke jagoranta, haɗin gwiwa da sauran ƙungiyoyin dake harka da, ko kuma taimakawa ayyukan agaji. Koda yake an yi shi ne don ayyukan agaji, amma kowace ƙungiya na iya amfani da CHS wajen inganta da kara ɗaukar nauyi na duk fannin ayyukansu tare da al'umma da mutanen da rikici ya shafa.

CHS sakamakon wani tsarin tattaunawa ne da neman shawarwari na duniya. Ya haɗa tare sanannun muhimman ka'idojin ayyukan agaji da alkawura. Waɗannan sun hada da, amma basu tsaya a iya:

- Dokokin Aiki na International Red Cross da Red Crescent Movement da Ƙungiyoyi masu zaman kansu (NGOs) da suke Bada Taimako a lokacin Bala'i ba;
- Ka'idar HAP akan Ɗaukar Alhaki da Gudanarwa da Inganci na 2010;
- Dokar People In Aid akan Dabi'u masu kyau wajen Gudanarwa da Tallafawa Ma'aikatan Agaji;
- Littafin Hannun Sphere akan Muhimman Ka'idoji da Sharuddan Aikin Agaji;
- Quality COMPAS;
- Alƙawarin Ƙungiya mai Jagorantar Ƙungiyoyin Agaji akan Ɗaukar Alhaki na Mutanen/Jama'ar da abun ya shafa (CAAPs); da
- Ƙungiyar Hadin Gwiwa don Tattalin Arziki da Ci Gaba (OECD) ta Sharuddan Kwamitin Taimakawa da Ci Gaba (DAC) don Kimanta Taimakon Bunƙasa da Agaji.

# Muhimman Ka’idojin Aikin Agaji akan Inganci da Ɗaukan Nauyi



## ii. Tsarin Muhimman Ka’idodin Aikin Agaji

CHS wani jerin Alkawura guda Tara zuwa al’umma da mutane da rikici ya shafa don faɗan abubuwan da za su iya tsammani daga ƙungiyoyi da ɗai-ɗaikun mutane da suke bada taimakon agaji. Kowane Alƙawari na tare da wani Sharadi na Inganci mai goyan bayan shi wanda zai nuna yadda ƙungiyoyin agaji da ma’aikatan ya kamata suna aiki don cika shi. Shi CHS an tsara shi kamar haka:

- alkawura Tara;
- tallafawa Ka’idar Inganci;
- Muhimman Matakai da za’a bi don cika Alkawuran; da
- Alhakin ƙungiyoyi don tallafawa daidaituwar da aiwatar da Muhimman Matakai ta bin tsari a ko’ina cikin ƙungiyar.

Muhimman Matakan da Alhakin Ƙungiyoyi, bi da bi, suna bayyana:

- abin da ma’aikatan agaji ya kamata su yi domin su gabatar da ingantattun shirye-shirye a kowane lokaci da kuma ɗaukan alhaki zuwa waɗanda suke ƙoƙarin taimakawa; kuma
- ka’idojin, hanyoyi da tsarurrukan da ƙungiyoyin agaji ke buƙatar samu domin tabbatar da ma’aikatansu sun samar da ingantaccen, da ɗaukan alhaki a lokacin taimakon agaji.

Kamus na kalmomin da aka yi amfani da su a CHS tare da ma’anoninsu na musamman a ƙarshen wannan takardar.

## iii. Aiwatar da CHS

Ƙungiyoyin da ke amfani da CHS sun yi niyyar cika dukkan alkawuran guda tara. A mafi karanci, ana sa ran su yi aiki don cigaba da inganta tsare-tsarensu, da gine-ginensu da dabi'unsu don tabbatar da Inganci da ɗaukar alhaki a duk ayyukansu na taimakon agaji. Koda yake, ƙungiyoyin da ɗai-ɗaikum mutanen da suke cikin aikin agaji suna da yawa. Suna buƙatar daukar mataki akan lokaci, da kuma sauya ayyukansu don daidaita shi da karfin da umurnin kungiyoyinsu har da matakin da yanayin rikicin da suka samu kansu ciki.

Idan ƙungiyoyi suna fuskantar matsaloli wajen cika Alkawuran nan Tara, ya kamata su, fadi hakan kuma su yi la'akari akan yadda za su magance matsalolin da ke hana su yin haka. Ya kamata ƙungiyoyi su koyi darasi daga yanayi irin waɗannan, ta samar da hanyoyin da za su iya shawo kan matsalolin da za su iya fuskanta.

Kowane bincike ko nazari akan aiwatar da CHS ya kamata ya zama bisa ga matakin da ƙungiyar take ƙoƙari wajen cimma Alkawura Tara din kuma ba wai akan ko an aiwatar da Muhimman Matakai da/ko an sauke Nauyin Ƙungiyar. Saboda haka Muhimman Matakai da CHS ke buƙata na neman an sauya shi bisa ga yanayin.

CHS ya shafi ƙungiyoyi da dai-ɗaikun mutane wanda:

- suke bada taimakon agaji kai tsaye ga garuruwa da mutanen da rikici ya shafa;
- samar da tallafin kudi, kayan aiki ko tallafin fasaha ga sauran ƙungiyoyi, amma ba sa shiga ayyukan ba da taimako kai tsaye; ko
- suna hada dukkan waɗannan hanyoyin.

An tsara CHS don masu aikin agaji su yi amfani da su ta hanya daban-daban, har da a matsayin wata hanyar:

- inganta ɗaukan alhaki ga al'umma da mutanen da rikicin ya shafa, da kuma karfafa ingancin hidimomin da ake musu;

- samar da shirin aiki don ci gaba da aiwatar da CHS da gyara;
- sa ido akan inganci da ɗaukan nauyi, ta amfani da CHS a matsayin tsarin goyon bayan ka'idojin ƙungiyar da fasaha;
- binciken kai da kara ingancin shirye-shirye;
- tabbatar ko shaida da bin dokokin ko ka'idodin, da kuma nunawa sauran wannan bin dokar; da kuma
- bincike, inda zai yi amfani, yadda tsarurrukan cikin gida da tallafawa ma'aikata suke cika matakai da nauyin ƙungiya da CHS ta bada

Ƙungiyoyin da suka yanke shawarar amfani da CHS ya kamata su karfafa shi ciki da wajen ƙungiyarsu.

Ƙungiyoyin da suke aiki da haɗin gwiwa, ya kamata su bayyana alƙawarinsu ga CHS, kuma su nemi fahimtar yadda abokan aikinsu[3] suke tunkarar Alkawuran nan guda Tara kuma suyi duk ƙoƙarinsu don aiki da su wajen aiwatar da alkawuran CHS.

## iv. Hakkoki

Kowane mutum ko ƙungiyar dake aikin agaji ana karfafa musu yin amfani da CHS kuma suna iya faɗan: "muna aiki don aiwatar da CHS". Ƙungiyoyi na iya faɗar cewa suna bin CHS kawai idan sun yi aikin tantancewa akan aiki da shi.

[3] Duba ma'anar a cikin jerin kalmomin.

## v. Aikin Bada Agaji na Ka'ida

Mutane su ne tushen aikin agaji. Abu na farko da yake sa a yi kowane taimako lokacin rikici shine ceton rayuka, rage wahalar da al'umma ke sha da tallafawa samar da hakkin rayuwa cikin mutunci.

Ƙungiyoyin da suke bada agaji sun aminta cewa ba da agaji shine ke kan gaba kuma suna ƙoƙari, don haka, da samar da taimakon agaji duk inda ake buƙata.

Ayyukan ba da agaji ya dogara ne akan dokoki huɗu da aka amince dasu a ko'ina[4]:

- Bil'adama: Dole a magance wahalar bil'adama duk inda aka gano. Dalilin aikin ba da agaji shine don kare rayuka da lafiya da kuma tabbatar da an mutunta 'Yan-Adam.
- Rashin nuna son kai: Dole ayyukan agaji su zama bisa ga buƙata kawai, da bada mahimmanci ga wadanda suka fi shiga cikin wahala da kuma ƙin ware kowa bisa ga ƙasa, kabila, jinsi, addini, matsayi ko ra'ayin siyasa.
- Yancin kai: Ya zama wajibi aikin agaji ya kasance bai da dangantaka da siyasa, tattalin arziki, rundunar jami'an tsaro ko wasu manufofi daban wanda wani zai iya riƙewa game da wurare inda ake aiwatar da ayyukan agaji.
- Ra'ayin Ba-ruwana: Ya zama wajibi ƙungiyoyin agaji kar su zaɓi wani gefe a lokacin yaki ko shiga kowane rikici na siyasa, kabila, addini ko ra'ayi.[5]

Dokokin ba da agaji su ne muhimman tushen dukannin ayyukan ba da agaji. Suna jagorantar ayyukan ba da agaji kuma aiwatar da su ya zama dole don banbanta aikin agaji daga sauran nau'in ayyuka da matakai. A cikin CHS, an haɗa dokokin ba da agaji cikin Alkawura, Sharuddan Inganci, Muhimman Matakai da Nauyin Ƙungiya.

Dokar Taimakon Agaji ta Ƙasa da Ƙasa, Dokar Hakkokin Yan-adam ta Kasa da kasa da Dokar ‘Yan gudun Hijira ta Ƙasa da ƙasa sun ba da asalin ka’idodin shari’ah game da kare ɗai-ɗaikun mutane da ƙungiyoyi, da kuma dangane da irin taimakon da wata kila za’a basu. Dokar Sphere akan Taimakon Agaji ta takaita muhimman ka’idoji bisa shari’ah wadanda suka fi mahimmanci akan lafiyar wadaanda rikici ya shafa.

Wadanda suke aiwatar da Muhimman Ka’idojin Aikin Agaji sun gano asalin nauyin jihohi da kuma sauran hukumomi masu amfani don kare da taimakawa wadanda bala’i ya shafa ko waɗanda akwai rikici da makamai cikin yankunansu. Bai kamata ayyukan agaji su rena waɗannan nauyin ba; tabbas, duk inda zai yiwu, ya kamata ya karfafa su.

[4] Ka’idojin ‘yancin bil’adama, rashin nuna son kai, yancin kai da ra’ayin ba-ruwana an samo su daga: asalin Ka’idojin Red Cross da Red Crescent Movement na Ƙasa da ƙasa da aka sanar a Vienna a 1965 a taron 20th International Conference na Red Cross da Red Crescent; United Nations (UN) General Assembly Resolution 46/182, 19 December 1991; da UN General Assembly Resolution 58/114, 5 February 2004.

[5] Wasu ƙungiyoyi, yayin ƙoƙarin ba da taimako ba tare da son kai ba da kuma ƙin zaɓan wani gefe a yaƙin, bisa la’akari da cewa ka’idar rashin goyon bayan kowa yana hana ba da shawarwari akan matsaloli game da ɗaukan alhaki da adalci.

# vi. Alkawura Tara da Sharuddan Inganci

1. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa sun samu taimako da ya dace da buatunsu
Ka'idar Inganci: Aikin agaji ya dace kuma yana da amfani.

2. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa sun samu damar taimakon agaji da suke buata a lokacin da ya dace.
Ka'idar Inganci: Aikin agaji na da tasiri kuma akan lokaci.

3. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa ba su zama cikin kunci ba kuma a shirye suke, ga juriya kuma basu kasance cikin hatsari ba sakamakon ayyukan agaji.
Ka'idar Inganci: Taimakon agaji na ƙarfafa albarkatun garin kuma ana gujewa tasiri mara kyau.

4. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa sun san hakkinsu da abinda yake nasu, suna da damar samun bayanai da kuma shiga yanke shawarwarin da suka shafe su.
Ka'idar Inganci: Aikin agaji ya dogara ne akan sadarwa, shigar da al'umma da karbar shawarwari.

5. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa suna samun damar hanyoyi masu tsaro da samun amsa don magance korafe-korafensu
Ka'idar Inganci: Ana karɓar korafi kuma a magance su.

6. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa suna samun taimako da aka daidaita, kuma masu karfafawa juna.
Ka'idar Inganci: Aikin agaji an daidaita shi kuma suna karfafawa juna.

7. Garuruwa da mutanen da rikicin ya shafa za su iya tsammanin ƙarin ingancin taimako tunda ƙungiyoyin agaji suna ɗaukar darasi daga ayyukansu da nazari.
Ka'idar Inganci: Ƙungiyoyin agaji suna cigaba da fahimta kuma suna gyarawa.



8. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa suna samun taimakon da suke buata daga kwararrun ma’aikata da masu sa kai da ake kula dasu da kyau.

Ka’idar Inganci: Ana tallafawa ma’aikata da yin aikinsu yadda ya kamata, kuma ba’a banbanta tsakaninsu.



9. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa na iya tsammanin cewa ƙungiyoyin da ke taimaka musu suna sarrafa albarkatu tare da inganci, yadda ya kamata da kuma ɗa’a.

Ka’idar Inganci: Ana amfani da kayan agaji yadda ya kamata kuma don manufarsu.

## vii. Alkawura, Matakai da Nauyi

### 1. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa sun samu taimako da ya dace da buatunsu.

Ka’idar Inganci: Aikin agaji ya dace kuma yana da amfani.

**Muhimman Matakai**

1.1 Kaddamar da tsari, mai manufa da nazari mai dorewa kan yanayi da kuma masu ruwa da tsaki.

1.2 Tsara kuma aiwatar da shirye-shiryen da ya dace bisa ga binciken buƙatu da aka yi ba tare da son kai ba[6] da hatsarori, da kuma fahimtar hatsarori da karfin rukunonin mutane daban-daban[7].

1.3 Sauya shirye-shiryen da canjin buƙatu, albarkatu da yanayi.

**Nauyin Ƙungiyar**

1.4 Ka’idoji suna alƙawarin ba da taimako ba tare da son kai ba sai dai bisa ga buƙatu da albarkatun al’umma da mutanen da rikicin ya shafa.

1.5 Ka’idojin suna ba da alkawura inda aka yi la’akari da bambancin al’umma, har da mutanen da aka ware ko mara karfi, da kuma don tattara bayani mai nuna bambancin al’umma.

1.6 An samar da hanyoyi don tabbatar da cigaba da nazari akan yanayi.

[6] “Bukatu” sun hada da taimako da kariya.

[7] Wannan ana nufin, misali ga: mata, maza, ‘yan mata, yara maza, matasa, da tsofaffi, da kuma wadanda ke da nakasa da ƙananan kabilu da basu daga cikin waɗannan.

## 2. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa sun samu damar taimakon agaji da suke buata a lokacin da ya dace.

Ka'idar Inganci: Aikin agaji nada tasiri kuma akan lokaci.

**Muhimman Matakai**

2.1 Tsara Shirye-shirye domin magance matsaloli yadda matakin da aka ɗauka zai yiwu kuma ya zama ba shi da matsala ga al'ummar.

2.2 Bada taimakon jin kai na gaggawa akan lokaci daidai-wa-daida, yanke shawarwari da ɗaukar mataki ba tare da bata lokaci ba.

2.3 A tura duk buƙatun da ba'a biya ba ga ƙungiyoyin da suka dace, kuma wadanda suke da ikon biyan bukatun, ko ayi kira da a magance su.

2.4 Yi amfani da fasahar da ya dace da kuma kyawawan ayyuka a dukkan ɓangaren aikin agaji domin haɗa shirye-shirye da bincike.

2.5 Sa ido akan ayyuka, tasirin da sakamakon taimakon agaji don sauya shirye-shirye da magance inda ba'a ƙoƙari.

**Nauyin Ƙungiyar**

2.6 Alkawurran shirin na daidai da karfin ƙungiyar.

2.7 Alkawuran gudanarwa sun tabbatar da:

a. sa ido da kimantawa mai tsari, da manufa kuma mai dorewa na ayyuka da tasirinsu;

b. kuma shaida daga wannan sa ido da kimantawa za'a amfani da su don sauya da gyara shirye-shiryen; da

c. yanke shawarwari akan lokaci tare da bayar da albarkatu yadda ya dace.

## 3. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa ba su zama cikin kunci ba kuma a shirye suke, ga juriya kuma basu kasance cikin hatsari sakamakon ayyukan agaji ba.

Ka'idar Inganci: Taimakon agaji na ƙarfafa albarkatun garin kuma ana gujewa tasiri mara kyau.

**Muhimman Matakai**

3.1 Tabbatar shirye-shirye suna karfafa albarkatu na gida kuma suna ƙoƙarin aiki don inganta jurewar al'umma da mutanen da rikicin ya shafa.

3.2 Yi amfani da sakamakon kowane bincike akan haɗari cikin al'umma da hatsarori da shirin da yake shi akwai don jagoran ayyuka.

3.3 Samar da cigaba ga jagoranci cikin gida da ƙungiyoyi a matsayin su ne waɗanda suke fara kawo agaji idan wani rikici ya taso nan gaba, su tabbatar da cewa an samu wakilcin mutanen da aka ware ko marasa galihu.

3.4 Tsara dabarun mika mulki ko fita a farkon matakan shirin aikin agaji da zai tabbatar da tasiri na gari mai dorewa kuma ya rage hatsarorin dogaro da taimako.

3.5 Tsara da aiwatar da shirye-shiryen da suke karfafa farfaɗowa da wuri daga bala'in kuma kuma ya amfani tattalin arzikin yankin.

3.6 Gano kuma ɗauki mataki akan illolin ainihi ko wanda ake tsammani akan lokaci da kuma ta hanya mai tsari, har da a ɓangarorin:
a. kare lafiyar mutane, tsaro, mutunci da hakkoki;
b. ci da gumi da cin zarafi ta hanyar jima'i da ma'aikatan ke yi;
c. dangantakar al'adu, jinsi, da zamantakewa da siyasa;
d. hanyoyin samun kuɗi;
e. tattalin arzikin yankin; da kuma
f. muhallin.

**Nauyin Ƙungiyar**

3.7 Ka'idoji, dabaru da jagorancin an tsara su don:

a. hana shirye-shiryen da za su cutar, kamar, alal misali, ci da gumi, cin zarafi ko ma'aikata su nuna bambanci cikin al'ummar da mutanen da rikicin ya shafa; kuma da

b. ƙarfafa albarkatun garin.

3.8 Tsarurruka sun kasance a wurin don kare duk wani bayanan kai da aka tattara daga al'umma da kuma matsalolin da mutane ke fama da su wadanda za su iya sa su cikin hadari.

4. Gariruwa da mutanen da rikici ya shafa sun san hakkinsu da abinda yake nasu, suna da damar samun bayanai da kuma shiga yanke shawarwarin da suka shafe su.

Ka'idar Inganci: Aikin agaji ya dogara ne akan sadarwa, shigar da al'umma da karbar shawarwari.

**Muhimman Matakai**

4.1 Samar da bayani ga al'umma da mutanen da rikicin ya shafa game da ƙungiyar, ka'idojinta, yadda yake tsammanin halayen ma'aikata ya zama, shirye-shiryen da suke aiwatarwa da abubuwan da suke da niyyar bayarwa.

4.2 Sadarwa a cikin harsuna, tsari da kafofin watsa labarai masu saukin fahimta, girmamawa da mutunta al'adun mutane daban-daban a cikin al'umma, musamman wadanda suka fi fuskantar hatsari ko ake nuna wa wariya.

4.3 Tabbatar cewa an hada da wakilci, da ya hada da kowa da aiki tare da shigar da al'umma da mutanen da rikici ya shafa a cikin dukkan matakan aikin.

4.4 Karfafa al'umma da mutanen da rikicin ya shafa su ba da shawarwari akan gamsuwarsu game da ingancin da tasirin taimakon da suka karba, da mayar da hankali musamman akan jinsi, shekaru, banbancin kabilun wadanda suka ba da shawarar.

**Nauyin Ƙungiyar**

4.5 An samar da hanyoyin ba da bayanai, da karfafa al'adar sadarwa a bayyane

4.6 An samar da hanyoyin shigar da al'umma da mutanen da rikicin ya shafa, tare da duba akan abubuwan da suka fi muhimmanci da hatsarin da aka gano a dukkan matakan aiki.

4.7 Sadarwar da ake yi a waje har da wadanda ake amfani da su don dalilin neman kuɗin tallafi, daidai ne, kuma suna da ɗa'a da kuma kalmomin girmamawa, da suke gabatar da al'umma da mutanen da rikici ya shafa a matsayin mutane masu daraja.

## 5. Gararuwa da mutanen da rikici ya shafa suna samun damar hanyoyi masu tsaro da samun amsa don magance korafe-korafensu.

Ka'idar Inganci: Ana karɓar korafi kuma a magance su.

**Muhimman Matakai**

5.1 Yi shawarwari tare da al'umma da mutanen da rikicin ya shafa game da tsara, aiwatarwa da bibiyar yadda ake magance korafe-korafe.

5.2 Ana maraba da karbar korafe-korafe, kuma a sanar yadda za'a iya samun damar tsarin da ire-iren matsalolin da za'a iya magancewa.

5.3 Gudanar da korafe-korafe ta hanyar da ya dace mai adalci kuma akan lokaci wanda yake bawa tsaron wanda ya kawo korafin mahimmanci da kuma duk wadanda abin ya shafa a dukkan matakai.

**Nauyin Ƙungiyar**

5.4 Hanyoyin magance korafe-korafe daga gararuwa da mutanen da rikici ya shafa a rubuce yake kuma akwai su. Tsarin ya kamata ya hada da shirin, ci da gumi da cin zarafi ta hanyar jima'i, da sauran nau'in nuna iko.

5.5 Al'adar ƙungiya inda ake ɗaukan korafe-korafe da mahimmanci kuma a ɗauki mataki akai bisa ga ka'idojin da hanyoyin da aka bayyana kuma an kafa.

5.6 Gararuwa da mutanen da rikici ya shafa suna da cikakkiyar masaniya akan irin halayyar da ya kamata ma'aikatan agaji su nuna, da ta hada da alkawuran da ƙungiyar tayi don ba da kariya daga amfani da dama da cin zarafi ta hanyar jima'i.

5.7 Korafe-korafen da basa cikin tsarin ƙungiyar ana tura su gaba zuwa wurin da ya kamata ta wata hanyar da ta dace da dabi'u masu kyau.

## 6. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa suna samun taimako da aka daidaita, kuma masu karfafawa juna.

Ka'idar Inganci: Aikin agaji an daidaita shi kuma suna karfafawa juna.

**Muhimman Matakai**

6.1 Gano matsayi, nauyi, karfi da ra'ayoyin masu ruwa da tsaki daban-daban.[9]

6.2 Tabbatar da cewa aikin agajin na tallafawa hukumomin kasar da na gida[10] da sauran ƙungiyoyin agaji.

6.3 Shiga cibiyoyin daidaita ayyukan da ya dace kuma haɗa kai da sauran don rage bukatun al'umma da kuma ƙara samar da ba da hidimomi na taimakon agaji gaba daya.

6.4 A yada bayanai masu mahimmanci ga abokan aiki, da ƙungiyoyin gamayya da sauran abokan aikin da suka dace ta sahihan hanyoyin sadarwar da suka dace.

**Nauyin Ƙungiyar**

6.5 Ka'idoji da dabaru sun hada da alƙawari a fayyace don daidaitawa da haɗin kai da sauran, har da hukumomin ƙasa da na gida, ba tare da sabawa dokokin ba da agaji ba.

6.6 Ana gudanar da aiki tare da abokan aiki ta yarjejeniyar da aka fayyace wadda take girmamawa duk manufar kowane abokin aiki, wajibai da yancin kai, kuma yana lura da ƙuntatawarsu da alƙawarinsu.

[9] Har da masu aikin agaji na gida, ƙungiyoyin agaji, hukumomin gida, kamfanoni da sauran ƙungiyoyin da suka dace.

[10] A inda hukumomin suke goya bayan rikicin ya kamata ma'aikatan agaji su yanke hukuncinsu bisa ga rashin dogara akan matakin, tare da sa al'umma da mutanen da rikici ya shafa a ransu wajen yanke shawarwari.

## 7. Garuruwa da mutanen da rikicin ya shafa za su iya tsammanin ƙarin ingancin taimako tunda ƙungiyoyin agaji suna ɗaukan darasi daga ayyukansu da nazari.

Ka'idar Inganci: Ƙungiyoyin agaji suna cigaba da fahimta kuma suna gyarawa.

**Muhimman Matakai**

7.1 Yi la'akari da abubuwan da aka fahimta daga aikin baya don tsara shirye-shirye.

7.2 A koya, a yi tunani sannan a aiwatar da canje-canje bisa ga sa ido da kimantawa, da shawarwari da korafe-korafe.

7.3 Yaɗa abubuwan da aka koya da kuma aka kirkiro a cikin gida, tare da al'umma da mutanen da rikici ya shafa, da kuma tare da sauran masu ruwa da tsaki.

**Nauyin Ƙungiyar**

7.4 An samar da tsarin kimantawa da koyo, kuma akwai hanyoyin da ake koyo daga abubuwan da suka faru kuma a yi gyara.

7.5 Akwai tsari domin adana ilimi da abin da aka koya, sannan ya zama abinda kowa zai iya samun sa ne a kungiyar.

7.6 Kungiyar tana taimakawa wajen koyo da kirkiro sabin abubuwa a aikin agaji tsakanin abokan aiki da kuma a ɓangaren gaba daya.

## 8. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa suna samun taimakon da suke buata daga kwararrun ma’aikata da masu sa kai da ake kula da su da kyau.

Ka’idar Inganci:[11] Ana tallafawa ma’aikata da yin aikinsu yadda ya kamata, kuma ba’a banbanta tsakaninsu.

**Muhimman Matakai**

8.1 Ma’aikatan suna aiki ne bisa tsari da abubuwan da ƙungiyar suka darajanta da kuma ta tsayayyun manufofi da ingancin aiki da aka amince da su.

8.2 Ma’aikata suna bin ka’idojin da suka dace da su kuma sun fahimci illar rashin bin su.

8.3 Ma’aikata suna hada kuma suyi amfani da kwarewar kai, fasaha da gudanarwa da ya kamata don taka rawarsu da fahimtar yadda ƙungiyar za ta iya tallafa musu da yin hakan.

**Nauyin Ƙungiyar**

8.4 Kungiyar tana da masu gudanarwa da ma’aikatan da za su iya gudanar da shirye-shiryensu.

8.5 Ka’idoji da hanyoyi don ma’aikata suna da adalci, a bayyane kuma babu nuna banbanci kuma suna bin dokar ɗaukan aiki na gida.

8.6 An ƙafa jerin abubuwan da aikin ya ƙunsa, manufofin aiki da hanyoyin shawarwari saboda ma’aikatan su samu cikakkiyar fahimtar abubuwan da ake buƙata daga wajensu.

8.7 An samar da dokokin aiki wanda yake kafa, mafi karancin, wajibin ma’aikaci kar yayi amfani da dama, ci zarafi ko kuma nunawa mutane banbanci.

8.8 An samar da ka’idoji don taimakawa ma’aikata da inganta dabaru da kwarewarsu.

8.9 An samar da ka’idodi don tsare lafiyar ma’aikata.

[11] Ma’aikata sune: duk wani wakilin ƙungiyar, da suka hada da na ƙasar, na kasa da kasa, ma’aikatan dindindin, masu aiki na ɗan lokaci kaɗan, hadda masu aikin sa kai da kuma kwararrun da ake tuntuba.

## 9. Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa na iya tsammanin cewa ungiyoyin da ke taimaka musu suna sarrafa albarkatu tare da inganci, yadda ya kamata da kuma ɗa'a.

**Ka'idar Inganci:** Ana amfani da kayan agaji yadda ya kamata kuma don manufarsu.

**Muhimman Matakai**

9.1 Tsara ayyuka kuma a aiwatar da su ta hanyar da za'a samu amfani da kayayyaki yadda ya dace[12], a daidaita inganci, farashi da lokaci a kowane matakin aikin.

9.2 Gudanar kuma a yi amfani da kayayyakin don cimma manufarsu, da kuma rage asara.

9.3 Sa ido kuma ba da rahoton kashe kuɗi akan kasafin kuɗin.

9.4 A lokacin da ake amfani da kayayyakin gida, a yi la'akari da tasirinsu ga muhalli.

9.5 A kula da hatsarin cin-hanci da rashawa sanan a ɗauki matakin da ya dace idan aka ga haka.

**Nauyin Ƙungiyar**

9.6 An kafa ka'idodi da hanyoyin amfani da gudanar da kayayyaki, har da yadda ƙungiyar za ta:

a. karba da bayar da kuɗi da kyaututtuka ta hanyar da ta dace kuma dai-dai da shari'a;

b. amfani da albarkatunsu ta yadda ba za a cutar da muhalli ba;

c. hana da magance cin-hanci, damfara, son rai, da almubazaranci;

d. gudanar da bincike akan kashe kudi, bin dokoki, da kuma ba da rahotanni a bayyane;

e. bincike, gudanar da rage hatsarori akai-akai; da

f. tabbatar da cewa karbar kayayyaki ba zai sabawa dokar yancin kai ba.

[12] Abinda aka kira “kayayyaki ko albarkatu” ya kamata a fahimce shi gaba daya, ya ƙunshi abubuwan da ƙungiyar ke buƙatar bayarwa don cimma manufarta har da amma ba iyaka ba da: kuɗi, ma’aikata, kaya, kayan aiki, lokaci, fili, kasa, ruwa, iska, halittu, da muhalli gaba daya ba.

## viii. Kamus

Saboda dalilin CHS, za'a yi amfani da waɗannan ma'anonin:

Ɗaukan Nauyi: tsarin amfani da iko yadda ya dace, lura da, kuma zama mai daukan nauyi, ga masu ruwa da tsaki daban-daban, da waɗanda amfani da wannan ikon zai shafa.

Garuruwa da mutanen da rikici ya shafa: ga baki dayan mata, maza, da yara maza da mata masu buƙatu, hatsari da karfi daban-daban kuma bala'i,rigingimu, talauci ko kuma wani rikici daban na wani wuri musamman ya shafe su.

Takarda: dukkan wani ma'ajin tattaunawa, yarjejeniya, shawarwari da/ko mataki wanda za'a iya sake wallafa shi.

Tasiri: yadda ayyukan ba da agaji suka cimma manufofinsu.

Yadda ya dace: yadda ake samun nasarar da tasirin shirye-shiryen taimakon agaji, har da na kaya da wanda ba na kaya ba, sakamakon abubuwan da aka sanya.

Shigar da Al'umma: tsarurrukan da ƙungiyoyi suke amfani da su don sanar, tattauna da/ko ba da damar shiga ga masu ruwa da tsaki da suke da ra'ayi da/ko wadanda abin ya shafa, domin tabbatar da an yi la'akari da damuwarsu, burinsu, tsammaninsu, bukatarsu, hakkinsu da damarmakinsu a wajen kafawa, aiwatarwa da yin gyara akan shirye-shiryen da za su taimaka musu.

Aikin agaji: matakin da aka ɗauka da nufin ceton rayuka, rage wahala da kare mutuncin Dan-Adam a lokacin da bayan wani rikici sakamakon bil'adama da bala'i, har da ɗaukan mataki don hanawa da shirya musu a gaba.[13]

Ƙungiya: wani abu da ya kasance akwai tsarin masu gudanarwa da mulki don aiwatar da CHS.

Partners: ƙungiyoyin da suke aiki ta haɗin gwiwa mai tsari domin cimma wani buri, tare da rawar da kowanne zai taka da nauyin su a bayyane.

Ka'idodi: rubutaccen bayanin manufa da ka'idodin yanke shawarwari.

Kariya: dukkan ayyukan don a tabbatar an girmamawa cikakken hakkin dukkan mutane ba tare da la'akari da shekaru, jinsi, kabila, matsayi, addini ko wani abu daban ba. Ya wuce ayyukan ceton rayuka da yawanci su aka saka a gaba lokacin taimakon gaggawa.

Inganci: gaba dayan siffofi da dabi'un taimakon agaji da ya tallafawa iyawa, akan lokaci, na gamsar da bukatun da aka sanar ko gani da abubuwan da ake tsammani, da girmamawa da mutunta mutanen da ake da niyar taimakawa.

Juriya: iyawar garuruwa ko al'ummar da masifa ta samu su jure, su hadiye, su yi hakuri kuma su farfado daga tasirin wani bala'i akan lokaci kuma ta hanyar da ya dace. Ma'aikata: sune duk wani wakilin kungiya, da suka hada da na kasa, na kasa da kasa, da ma'aikatan dindindin ko na dan lokaci kaɗan, masu aikin sa kai da kuma kwararrun da ake tuntuba.

[13] Kamar yadda aka bayyana a ALNAP Evaluation Humanitarian Action Pilot Guide, 2013, p, 14.

**Muhimman Ka'idodin Aikin Agaji akan Inganci da Ɗaukan Alhaki** (CHS) ta bada Alkawura guda Tara wadanda ƙungiyoyi da ɗai-ɗaikum mutanen da suke aikin agaji zasu yi amfani da su wurin kyautata inganci da tasirin taimakon da suke bayarwa. Yana kuma tamaikawa wajen ɗaukan alhaki ga al'ummomi da mutanen da rikicin ya shafa: sanin nauyin da ya rataya a wuyan ƙungiyoyi zai taimaka wajen dorawa kungiyoyin laifi idan suka kasa basu hakkinsu.

A matsayin muhimman ka'ida, CHS ta bayyana abubuwan da suka zama dole don yin aikin agaji mai ka'ida, inganci sosai da kuma ɗaukar alhaki. Ƙungiyoyin bada agaji zasu iya amfani da shi a matsayin wata ka'ida ta daidaita hanyar tafiyar da tsarin su. Kuma za'a iya amfani da shi a matsayin wani hanyar tantance ingancin ayyuka.

CHS sakamakon wani tsarin tattaunawa na wata 12 a matakai uku da HAP, People In Aid da Shere Project suka jagoranta kuma a in da daruruwan mutane da ƙungiyoyi suka yi nazari akan abinda CHS ya ƙunsa kuma suka jarraba aiki da shi a manyan ofisoshinsu da kuma fagen aiki.

corehumanitarianstandard

@corehumstandard

www.corehumanitarianstandard.org | info@corehumanitarianstandard.org